ARDP

Arewa Research & Development Project

# TARIHIN TUSHEN KYAWAWAN AL'ADU NA SHUGABANCI DA YAKI DA CIN-HANCI DA KUMA TABBATAR DA ADALCI A NIJERIYA TA AREWA.

# HISTORICAL FOUNDATIONS OF LEADERSHIP VALUES ON ANTI-CORRUPTION AND SOCIAL ACCOUNTABILITY IN NORTHERN NIGERIA

# DARAJA'A NƎM FUWUMA JAMABE'E DUKSHINZƎ KƎLA JIREGANA GƎRTƎ'A HAKKU JAMAYE'A KAKKALRO SAOBE SURO YALA NIGRIABE

## TARIHIN TUSHEN KYAWAWAN AL'ADU NA SHUGABANCI DA YAKI DA CIN-HANCI DA KUMA TABBATAR DA ADALCI A NIJERIYA TA AREWA.

Akwai damuwa da yawa game da tasirin cin hanci da rashawa a harkokin mulkin jama'a, wanda ya kasance ɗaya daga cikin manyan matsalolin wajen samar da kyakkyawan sakamako wajen samar da ayyukan more rayuwa a cikin ƙasashe masu tasowa. An fassara cin hanci da rashawa a matsayin 'yin amfani da ofishin gwamnati don tara dukiya'.Tare da yin amfani da karin magana, "babakere tare da karfin ikon da babu iyaka", Robert Klitgaard (masanin al'amuran mulkin jama'a) ya laƙanta cin hanci da rashawa a lokacin da wani zaiyi babakere a kan al'amari ko aikin jama'a, tare da ikon zartarwa ko hanawa ba bisa wata hujja ba. Saboda haka, rashin nuna gaskiya a cikin al'amuran jama'a, da ƙin bin hujjoji daga shugabanni da kange al'umma daga bin sawun al'amuran mulki shine ke haifar da yanayin cin hanci da rashawa. Hakan ne ke nuni da cewa cin hanci da rashawa yana faruwa ne sakamakon mumunar tafiyar da mulkin jama'a.

Saboda haka, sinadarin yaƙi da cin hanci da rashawa yana da nasaba da tsarin samar da dabarun zamantakewar al'umma ta samar da sa idon al'umma domin tallafawa da kuma karfafa shugabanci mai kyau. Manufar kyakkyawan shugabanci yana ɗaukar nauyin lissafi game da tsarin zamantakewa, inda 'yan ƙasa da suka zabi gwamnati zasu sa idon cuɗanya mai ma'ana a akan shugabannin mulki - wanda shine maƙasudin tsarin demokraɗiyya - domin kula da haƙƙoƙin jama'a da samun ingantattun ayyukan more rayuwa. Sa idon al'umma tare da cuɗanya da shugabanin mulki zai rage, ko kuma ya hana, aukuwar cin hanci da rashawa. Wannan shine ke nuna dangantar sa idon al'umma da yaƙi da cin hanci da rashawa.

A bisa jinƙan al'ammura, daulolin mulkin na nahiyar tsakiyar Sudani, waɗanda sune suka haifi Arewacin Nijeriyar wannan zamani, sun samar da tanade-tanaden Shari'a da ɗabi'un jagoranci game da yaki da

cin hanci da rashawa. Saboda haka, a cikin aiwatar da wannan aikin gangamin a kan yaki da cin hanci da rashawa da kuma inganta tsarin sa ido a zamantakewar al'ummar Arewacin Nijeriya, musamman jihohin Borno da Zamfara, Cibiyar bincike da bunƙasa Arewacin Nijeriya (ARDP) taga mahimmancin raba wasu ƙasidu waɗanda shugabannin Daular Usumaniyar Sakkwato da Daular Borno suka wallafa a kan shugabancin al'umma da siyasarsu.

Mun yi la'akari da cewa fahimtar tarihi na tushen jagoranci a kan cin hanci da rashawa da kuma inganta zamantakewar jama'a zai yi amfani wajen taimakon ƙoƙarin ƙungiyoyin wannan zamani wajen bayar da nasu agaji ga gwamnatoci wajen yaƙi da cin hanci da rashawa a harkokin gwamnati. Saboda haka, hanyoyin da za a tsara domin sa idon al'umma zasu samar da hanyoyin cuɗanya da gwamnati inda kungiyoyin al'umma za su taimaka wajen gudanar da harkokin jama'a cikin ayyukan gwamnati.

**(Shugabannin aiwatarwa, Na ƙungiyar ARDP)**
ShirinYaƙi da Cin Hanci da Samar da Hanyoyin Gyaran Al'amurra a Arewacin Nijeriya.

## HISTORICAL FOUNDATIONS OF LEADERSHIP VLUES ON ANTI-CORRUPTION AND SOCIAL ACCOUNTABILITY IN NORTHERN NIGERIA

There is an overwhelming concern on the impact of corruption in public affairs, which represents one of the major obstacles to achieving effective social service delivery in developing countries. Corruption is generally understood as the 'misuse of public office for private gain'. Using the formula "monopoly plus discretion minus accountability", Robert Klitgaard sees corruption when someone has monopoly power over a good or service, has the discretion to decide whether one receives it and how one gets, and is not accountable. Hence, the absence of transparency in the conduct of public affairs, the refusal of those in power to account, and the lack of meaningful citizen participation in decision-making contribute to the conditions for corruption to happen. Such conditions show that corruption occurs as a consequence and manifestation of bad governance.

Thus, anti-corruption inherent monitoring strategies begets social accountability as the framework of action to support and sustain good governance. The concept of good governance carries with it connotations of social accountability, where citizens and citizens groups constructively engage government – which, in essence, is what democracy is all about – for the purpose of monitoring the use of public resources towards improved delivery of services, community welfare, and protection of people's rights. Social accountability is thus to provide the constructive engagement between citizens and government through civil organizations' monitoring, which could minimize, if not pre-empts, corruption. This explains the logical connection between anti-corruption and social accountability.

Mercifully, the pre-colonial polities in the Central Sudan, out of which modern Northern Nigeria emerged, embodied the ideals (policies) and programs about leadership values on anti-corruption and social accountability. In its implementation of the project on Anti-

Corruption and the Promotion of Social Accountability in Northern Nigeria, with particular attention to Borno and Zamfara States, the Arewa Research and Development Project (ARDP) finds it extremely important to share some extracts propounded by the leadership of the Sokoto Caliphate and Borno Empire on political leadership, anti-corruption and social accountability.

We envisioned that understanding historical foundations of leadership values on ant-anti corruption and promotion of social accountability will rhyme with the efforts of donor agencies and governments towards looking at new ways the civil society can assist in fighting corruption in public administration. Thus, social accountability mechanisms will revolve around citizen engagements with government in a systematic manner to provide and sustain horizontal accountability in the conduct of public affairs.

**(The ARDP Co-ordinating Team)**
Project on Anti-Corruption and Promotion of Social Accountability in Northern Nigeria.

**DARAJA'A NƎM FUWUMA JAMABE'E DUKSHINZƎ KƎLA JIREGANA GƎRTƎ'A HAKKU JAMAYE'A KAKKALRO SAOBE SURO YALA NIGRIABE**

Ku suro lardə'a fuwutə hadizana soye letəgəramza rumiya awo karəgə kuttabe kura fal ndusoye kəladən zəktəna faldə shima lamar kura'a yamaye soye jiregana suro jama'a notonzabedə.Shi jire adə alama kərta au razəgə jamabe kaune liwunəmro yikke gairo shagozana.Samma dukshinzə dəye, wumangalwo'a kam harribtə'a shi ganabe dəa nzərfatto'a bas. Ilmuma laa Robert kligaard dəye guljin dən wono-shi jire-gana adə alama kambe duno kərmaibe faidatə kam soa ratsəgəiya daji am anyi hakkinza sawandənyi yaye awo sha zəktsənaba balle njimalta. Nangadəro suro jamaro chiida kəndoben jire fəletəbaso sandi kurawa jamabe sodəye kəla jire ganaben bam naptaso, kuru am jire'a soa yikkəm chida ngəla kəndobaso dəye səkkə daryenzə affinzə yaye kal-lan kəlagotin.

Daji na-allan ruwiya shi jire-gana adə kambowoso, nəm adal-ba fərtəworo isə gumnati dəa bannajin. Nangadəro ku rumiya kərigə-jire-gana gərtəbe kəndodə shima dea nəm adalla, chida ngəla'a tadaro sambin.Ndaran yaye ferno gumnati adalbedə tadanzə də nəm adalla hakku jamaye kakkalro kənjo'a. na donyi karapka'a ngəla-ngəlaso chiza kəla kəlza lamar jamaro kakkalro chida kəndobe də sandiya katennaro waljin.Daji adəma gumnati nəm kam-be jamaye tawatta'aye zarnzədəwo. Shi hakku jamabe tawatta'adəye sambisoro ndəwu ndi kate gumnatiya jamabe'a də shima karapka'a jamaye jili-jili soa katedəro yikkem namtə ndəwubero walzai. Daji adə-tədiya lamar də kaaye lai-kanəmbe-lairo waljin.

Na-allan daji jire-ganaso, jama haribtəsoye baro waljin. Kangesəbe halnzə sədənyi'a yim zaman nasara'abe dən lardəa Afrikabe hatta yala'a Nijeriayabe kuyema suronna adəlan, kəla nəm adalye mbeji, jireye mbejiye dən affiso kakalro bejin karrakəla futu chanjire tədənadən missal gonəm kakkalro letəben karapka kulashi's chidaa yalaa lardəyero deo'aye shiro Arewa Research and Development

Project gulzain dəye kəla kərye'a alama Borno gai, Zamfara gai ladən jire tədəben, misalwa gumnati adin Islambe kurebe alama daula Sokotobe shiro Sokoto Caliphate gulzain dəgai daula kanem bornobe shiro Borno Emirate gulzai dəgaiso lan misalwa gowono.

Nangadəro kurundə ladənna, hal jamasoa kakkalro notəm jire tawattagabe dən karapkaa hakku jamabero mbəltama soa gonəm katedəro yikkodə, awo zaumaro kakkalye kuru sandənayero chure. Shi hakku jamaye soa kakkalro tawttaa adə karapkaa soa katedəro yikkodəye gana-ganamen awoa kakkalgənyi soa sasein kuru lairo sikkənne, kuru shi gumnati dəyero shima kakkalwoye, shima herwoye.

**(Bayan adə na karapka kulashi'a chida'a ngəla yalaa lardəbero deoye shiro Arewa Research and Development Project (ARDP) yen təwando.)**

# HAUSA VERSION

## KASHIN BAYAN SHUGABANCI

### 1. Shugabanci A Matsayin Amanar Allah

Babu shakka, mulki wakilci ne daga Allah, kuma amana daga Annabin Allah. A duba irin martabarsa da kuma irin nauyinsa. Idan shugaba ya bi hanyar madaidaiciya sai taqawa ta yi zarra a kan bukatunsa na duniya, idan kuwa ya fandare sai taƙawarsa ta zama baiwar buƙatunsa na duniya. Saboda haka ka ji tsoron Allah (kila ka yi nasara) ka kwana da sanin cewa "Duk wani rai zai-ɗanɗani mutuwa, kuma za ka karɓi cikakken sakamakonka a ranar hisabi. Saboda haka duk wanda aka 'yanta daga wuta, aka kuma shigar da shi Aljanna to lallai ya yi galaba, domin kuwa wannan duniyar ba kome ce ba illa hanyoyi na yaudara".

(Daga Shehu Abdullahi dan Fodiyo, wanda ya tsakuro daga Imam Muhammad Ibn Abdulkarim al-Maghili. (1504): a cikin littafinsa *Diya ul-Hukkam*, Yamusa 1990:8).

### 2. Shugabanci A Matsayin Abin Bayyanawa Dalla-Dalla

Ka san da sani yaɗan'uwana, cewa ɗaya daga cikin babban bala'in da zai Faɗa wa bawa (na Allah) shi ne ya zama shugaba, domin buƙatar ya yi cikakken bayanin muƙamin. A ƙa'ida kowane bawa zai yi cikakken bayanai akan kalamansa da ayyukansa da kuma mu'amalolinsa. Idan an naɗa shi shugaba, to lallai banda nauyi ayyukansa da ke kansa, za a kuma buƙaci bayani a kan waɗanda ya shugabanta. To idan ba zai iya sauke nauyin da ke kansa da kyau ba, ya ya matsayinsa zai kasance ke nan idan aka nemi ya yi bayani dalla-dalla a kan ayyukan waɗandà ya shugabanta? A kan wannan ne aka ce. "Duk wanda Allah ya dankwafar to ya gode masa, domin kuwa ya rage masa wahalar nauyi wanda lallai sai ya yi bayaninsa dalla-dalla. Wannan yana cikin waɗanda ba su da bayanin da za su yi da yawa, illa dai rigingimun duniyar nan, wadda babu wani abu a cikinta illa

damuwa, idan kuwa ba haka ba, babu abin da zai samu a lahira illa azaba. A dalilin haka ne Manzon Allah tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya ce " kuna so in gaya maku wani abu a game da shugabanci da kuma abin da yake nufi?" Sai (masu sauraronsa) suka ce "E, ya Rasulullah," sai kuma yace "farkonsa shi ne zargi, kashi na biyunsa shi ne nadama, kashi na uku shi ne azaba a ranar tashin ƙiyama".

*(Sarkin Musulmi Muhammad Bello, a cikin Usul al-Siyasa, (Wallafar) Yamusa 2004:11)*

A cikin Al-Janharah an ruwaito cewa Ali b. Abi Talib ya ce, "na ga Umar b. al-Khattab da sassafe a kan wata dabba sai na ce da shi "ya Amirul Muminin, ina za ka je?" Sai kuma ya amsa "wani raƙumi da aka bayar sadaka ya ɓace shi ne nake neman sa". Sai na ce, "ka aza wa Halifofin bayanka aiki ya Amirul muminina da wannan abu" sai ya ce "kada ka zarge ni ya Abul-Hasan domin na rantse da wanda ya aiko Muhammad (Annabi) da annabci cewa idan tunkiya za ta ɓace a gaban tekun "Euphrates" za a tambayi Umar ya yi bayani a kanta a ranar tashin ƙiyama, domin kuwa babu wani girma ga shugaban da ya ki kulawa da dukiyar musulmi".

### 3. Shugabanci A Matsayin Alheri

Muhimmancin shugabanci da kuma nauyin muƙamin sun samo asali ne daga abin da aka ruwaito daga Manzon Allah, tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi, wanda ya ce, "adalcin shugaba na rana ɗaya, yafi ibadar wani wanda ba kowa ba ta shekara saba'in."

Manzon Allah, mafi kyawon rahama da mafi ɗaukakar gaisuwa su tabbata a gare shi ya ce, " mutumin da ake ji da shi kuma wanda ya fi kusa da Allah shi ne shugaba mai adalci, amma mutumin da Allah ya fi ƙi kuma wanda ya fi nesa da shi, shi ne azzaalumin shugaba". Manzon Allah, tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya ce, za'a

rubuta kyawawan ayyukan adalin shugaba da daraja, adadin ayyukan dukkan talakawansa, kuma ladar duk wata salla da ya yi za a ba ta darajar salloli 70,000 da wasu suka yi. Tunda haka ne babu abin da yafi ga bawan Allah kamar a bashi mukamin shugabanci. Allah ya sanya sa'a ɗaya ta rayuwar shugaba ta yi darajar rayuwar wani mutum gaba ɗayanta. Duk wanda bai yi la'akari da muhimmancin wannan gata ba, ya damu kansa da zalunci to Allah zai sashi cikin maƙiyansa.

*(Sarkin Musulmi Muhammad Bello, Usul al-Siyasa, Yamusa 2004: 11-12)*

### 4. Shugabanci A Matsayin Yi Wa Mutane Hidima

Duk wanda Allah ya jarabce shi da muƙami *(wilaya),* to ya yi aiki tuƙuru wajen sauke nauyin. Koda yake yana iya zama fitina duk da haka yana ɗaya daga cikin manyan alheri. Duk mutumin da ya sauke nauyinsa da kyau ya kuma yi godiya ga Mai Rahama to zai samu farin ciki marar ƙarewa, irin wanda ba a taɓa yin irinsa ba. Ta ɓangare guda kuwa duk mutumin da ya kasa sauke nauyinsa, da godewa mai bayarwa, to zai shiga fitina marar iyaka, wadda sai dai kurum a kwatanta ta da kafirce wa Allah mai girma da ɗaukaka.

*(Sarkin Musulmi Muhammad Bello, Usul al Siyasa, Yamusa 204:11)*

Lallai shugaba ya kula da jin daɗin mutane. Kada ko da wasa shugaba ya ɗauka shi ne ya mallaki lardin da aka ce ya shugabanta ta yadda ƙasar ta zama ta ƙashin kansa, wadda zai iya bayarwa ga wanda yake so, kuma ya hana wanda ya so. Wannan irin aikin zamanin jahiliyya ne. Ya san da sani cewa an ba shi amanar kula da mutane ne domin ya kula da addininsu da kuma buƙatunsu na duniya.

*(Shehu Abdullahi Ibn Fodiyo, Diya'ul Hukkam fi ma hukum wa alaihim min al ahkam 1807, Yamusa 1990:13)*

Kula da jin dadin mutane ya fi warkarwa fiye da amfani da ƙarfi. An faɗa cewa mulkin shugaba shi ne mutuncinsa, ƙarfinsa shi ne rashin nuna bambanci, dukiyarsa kuwa ita ce kula da jin daɗin mutanensa. Ba a yin nasara da yin yankan ƙauna, ba a yin mulki babu ilmi, kuma ba a yin shugabanci da ɗaukar fansa.

*(Shehu Usman Ibn Fodiyo, Bayan Wujub al-Hijra. El Masri, 1978:150)*

## 5. Sugabanci A Matsayin Adalci.

Shugaba yana samun nasara ne a kan maƙiyansa kwatankwacin adalcinsa ga mutanensa, ana kuma yin galaba a kansa wajen fafitikarsa daidai irin zaluncinsa.

*(Shehu Usman Ibn Fodiyo Bayan, Wujab al-Hijra, El masri, 1978: 150)*

Dole ne shugaba ya tabbatar ya yi adalci, kuma ya kyautata. Adalci shi ne ya ba kowa haƙƙinsa. Duk ɗaya ne ko wannan haƙƙi an samo shi daga kansa ko kuma daga wasu. Kyautatawa kuwa ita ce ya yi abu mai kyau, ya bada kyauta daga dukiyarsa amma ba daga ta wani ba.

Ana yin adalci yadda ya dace idan ya duba koke-koken masu husuma daidai wa daida; ta yadda ya karɓe su, da yadda suka zauna a gabansa, da yadda ya dube su, da yadda ya yi musu jawabi, da dukkan sauran al'amurra da suka shafe su, ba tare da fifita wani sashe ba. Kada ya amsa gaisuwar wanda ya gaida shi da nuna tsananin jin daɗi da sanayya, kuma kada ya yi magana da shi fiye da kima, sai dai fa idan ya fahimci cewa mutumin ba shi cikin waɗanda ake husumar da shi, kuma amsar da ya bayar ba za ta jawo wani abin da aka haramta ba.

Dole ne shugaba ya zauna a gaban jama'a a kullum, yadda mutane musamman mata da yara za su iya kai wa gare shi. Bai wadatar masa ba, ya dogara ga waɗanda ya naɗa (su kula da al'amurran jama'a) irin su alƙalai da sauran ma'aikatan gwamnati. Domin kuwa kila ƙorafe-

ƙorafen mutanen a kan waɗannan mutanen ne, domin haka tilas ya yi musu adalci. Idan ba haka ba kuwa sai ya zama tamkar kwaranga ga masu ita, ko kuma mai riƙe ƙahunnan sanuwa ga mai tatsa. Halifofi (Allah ya jiƙan su) sun cire ma'aikata masu gaskiya, a sanadiyar kuka da aka yi a kansu, kuma abin da suka yi, ya yi kama da tausayawa. Kyautatawa ita ce ruhin mulki, rashinta shi kansa zalunci ne.

*(Shehu Abdullahi dan Fodiyo, a cikin Diya ul-Hukkam, Yamusa 1990: 9 – 10)*

Na furta cewa, nasara daga Allah ta ke, Allah ya ce kada ku ɗauka cewa Allah bai sane da abin da masu mummunan aiki suke yi. Yana jinkirta masu ne ya zuwa ranar da idanawa za su bubbuɗe cikin kiɗima. Diya al-khulafa, ya ce: Wannan ayar cikakken gargadi ne ga azzalumai kuma cikakken rarrashi ga waɗanda ake zalunta. Ka'b ya taɓa ce wa Abu Huraira, an faɗa a cikin Attaura cewa. "za a yi rugu-rugu da gidan azzalumi." Sai Abu Huraira ya amsa da cewa, haka ma an faɗa a littafin Allah cewa: "Waɗancan su ne gidajensu sun ragurguje domin ɓarnar da suka aikata. Zalunci shine abu mafi sauƙi wajen hana samun falalar Allah da kuma jawo bala'i. Ibn Abbas ya ruwaito Manzon Allah ya ce, "ku yi hattara da addu'ar wanda aka zalunta, domin babu shamaki tsakaninta da Ubangiji." Abu Huraira ya ruwaito cewa Annabi ya ce, "wanda ya zalunci ɗan'uwansa ta mutuncinsa ko dukiyarsa, to lallai ya gyara kwatankwacin zaluncin da ya yi kafin ranar da babu dirhami ko dinari. Domin kuwa a wannan ranar idan mai laifin yana da wani aikin alheri, za a rage su daidai yawan zaluncin da ya yi. Idan ba shi da wani aikin alheri, za a ba shi wasu munanan ayyukan wanda aka zalunta." Sa'id Ibn Zaid ya ce ya ji Annabi ya ce, "duk wanda ya ƙwace wani ɗan taƙin ƙasa, za a kaurara taƙin ya kai girman ƙasa ta bakwai a rataya masa ita a wuya". Anas ya ruwaito Annabi ya ce, "ku taimaka wa ɗan'uwanku walau shi ne mai zalunci ko wanda aka zalunta". Sai ya tambaya cewa, "ya

Manzon Allah, za mu taimaka masa idan an zalunce shi, to amma ta yaya zamu taimaka masa idan shi ne ke yin zaluncin?" Sai ya ce, "ta hana shi."

An ce wani shugaba ya rubuta waɗannan layuka na baitoci a kan darduma:

*Kada ka yi zalunci idan kana da muƙami*
*Domin yin žalunci yakan sa tagumi.*
*Idanunka na gyangyadi wanda aka zalunta na zaune.*
*Yana la'antarka, kuma Allah na sane*
*Addu'ar wanda aka ƙwara, lallai ta kai ka*
*Halin ƙunci da muzantawa da kuma damuwa*

Bilal ya ce, ka ji tsoron Allah a kan mutumin da ba shi da mataimaki sai Allah. An ruwaito Annabi ya ce, Allah ya ce. "Fushina ya fi tsanani a kan mutumin da yake zaluntar wanda ba shi da mataimaki illa ni".

*(ShehuUsman Ibn Fodiyo, Bayan Wujub al-Hijra, El Masri 1978:140)*

Annabi ya ce, "duk mutumin da ya yi sulhu a tsakanin abokan adawa biyu, kuma ya yi zalunci (to lallai ya san da sani) la'anar Allah na a kan duk mutane azzalumai." Ya kuma ce, "akwai mutane uku waɗanda Allah ba zai dube su ba a ranar tashin ƙiyama; maƙaryacin mai mulki da mazinacin tsoho, da talaka mai ji da kansa" Ya kuma ce da sahabbansa "Wata rana zata zo da za kuci wasu sassa na Gabas da na Yamma, dukkansu za su kasance a hannunku, kuma dukkan waɗanda za su amshi shugabanci za su shiga wuta, sai fa waɗanda suka ji tsoron Allah mai girma da ɗaukaka suka yi taƙawa, kuma suka yi aikinsu tsakani da Allah".

Annabi tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi, ya kuma ce, "duk wani bawan Allah da aka naɗa ya shugabanci al'amurran mutanensa, amma ya yi cuta, ko ya ƙi ya basu shawara mai kyau, ko ya tausaya masu, to Allah zai hana shi shiga Aljanna." Ya kuma ce, "duk wanda aka naɗa ya shugabanci al'amurran musulmi, amma ya ƙi ya kare su tamkar yadda zai kare iyalansa, to lallai zai sami mazauninsa a wuta". Ya kuma sanar cewa, "mazaje biyu daga al'ummata ba zasu sami cetona ba: azzalamin shugaba da kuma fanɗararren zindiƙi wanda a koda yaushe yake saɓa wa dokoki."Ya kuma ƙara da cewa, "wanda zai sha uƙuba mafi-tsanani a ranar tashin ƙiyama shi ne shugaba mai kama-karya".

*(Sarkin Musulmi Muhammad Bello, Usul al-Siyasa, Yamusa, 2004:11-12)*

### 6. Shugabanci A Matsayin kyakkyawan Abu

Kyakkyawan aiki shi ne darajar hali. Tunda Ubangiji ya sani ba kowa ne yake wadata ta adalci kaɗai ba, yana buƙatar kyakkyawan aiki wanda ya fi adalci martaba sai Ubangiji ya hada su tare. A taƙaice shi ne talakawa suna da rakuni iri uku ne ga shugaba: tsofaffi; da ƙanana; da kuma, na tsaka-tsakinsu. Tilas ne shugaba ya kula da tsofo tamkar uba, na tsakiya a matsayin ɗan'uwa, ƙarami kuma kamar ɗa. Saboda haka ya girmama babansa, ya kyautata wa ɗan'uwansa, kuma ya nuna ƙauna ga ɗansa".

*(Shehu Usman Ibn Fodiyo, Bayan Wujib al-Hijra, El-masri, 1978:66)*

### 7. Shugabanci A Matsayin Tanajin Abu Ma Fi Kyau

Idan Ubangiji na son jama'a sai ya mika shugabancinsa ga mutane mafi kyau daga cikinsu. Sai kuma ya basu waɗanda za su taimaka masu. Irin waɗannan shugabanni su ne za su jagoranci jama'a ta hanyar da ta dace, kuma su yi ayyuka daidai-wa-daida. Za su nemi shawarar mutane masu ilmin da ya dace kan warware matsaloli. Za su

nemo muhimman mutane, da mutane masu ilmi da kwararru su taimaka ta fannoninsu. Za su darajta addu'oin mutane masu taƙawa, domin al'ummar ta ci-gaba ta kowacce fuska. Irin waɗannan shugabanni za su ƙara girma ga matanen da suka cancanta, su hana wa waɗanda ba su kamata a ba su ba.

*(Sarkin Musulmi Mahummad Bello, Ifadat al-Ikhwan, Tukur, 1999:77)*

**8 Shugabanci A matsayin Hanyar koya Tarbiyya**

Lallai shugaba ya umurci mutanensa su yi adalci, da kyawawan ayyuka, kuma su guje zaluntar juna, su so abubuwa kyawawa su kyamaci munana. A gwari-gwari dai kyawawan halayen shugaba da ayyukansa hotone na kyawawan ayyukan mutanensa da halayensu. Saboda haka idan suka yi ɗa'a ga Ubangijinsu mai Rahama da Girma da Ɗaukaka, sai ya sanya tausayi a zukatan shugabanninsu, su kyautata masu. Amma idan akasin haka ne, suka ƙi bin umurnin Ubangijinsu suka nemi su yi fasadi a duniya, sai ya sanya shugabanninsu tursasa masu, a karshe su zalunce su. Allah Mai Girma da Daukaka yace "Sai muka kyale wasu daga cikin maɓarnatan suka mulki wasu (sakamakon abin da suke so su mallaka." An kuma ruwaito a Hadisi cewa za a mulke ku "kwatankwacin yadda kuke".

*(Sarkin Musulmi Muhammad Bello, Usul al-Siyasa, Yamusa 2004:16-17)*

**9. Shugabanci A Matsayin Hali Abin Koyi.**

Mulki tarnaki ne ga kwamacalar zukatan mutane. Saboda haka duk wani shugaba ya rungumi halin girmamawa, walau a birni ko a kauye. Ka nuna sonka ga abu mai kyau, da kuma mutane na gari; ka nuna ƙiyayya ga fasadi da mutane masu alfasha. Ka ƙawata jikinka, ka shafa wa lumfashinka turare, ka yi tufafi masu ado da ƙyale-ƙyale da aka halasta, ba tare da koyi da wasu ba, ko ta kwashe kuɗin baitul mali a tatuke shi. Kada ka zuba wa kanka zinari ko tagulla ko tulin

siliki domin yin haka abin kunya ne, abin da aka ƙi ne, kuma bai dace ba. Ka zauna a harde idan ka zauna. Ka natsu iyakar iyawarka, babu mutsu-mutsu ko da da hannu, idanawanka su riƙa kallon ƙasa-ƙasa suna dubi mai ma'ana, kuma ka yi kallo a tsanake. Ka tunkari mutane cikin mutunci kada ka buɗe bakinka ko da hamma za ka yi. Idan hamma ta kama ka, faɗi sunan Allah za ta wuce. Amma idan ka bari kwaɗayin ya ci ƙarfinka, to ka rufe bakinka da bayan daya daga cikin hannuwanka. Wani sha'iri (marubucin waƙa) ya ce :

Kada ka taɓa yin dariya da ƙarfi
Domin makafi kurum ke yin haka.
Ta ƙarfafa wa makantarsu.
ka rungumi son yin shiru ko yaushe
Domin mai surutu bai cika kuɓuta ba
Idan har sai ka ce ƙala to taƙaita a tsanake
ƙasƙantar da kanka domin lokacin mutuwa
Sai ka yi wa kanka kiyamul laili.

*(Shehu Abdulahi Ibn Fodiyo, wanda ya tsakuro daga ImamMuhammad Ibn Abdulkarim al-Maghili (1504) a Yamusa 1975: Tsakuren naan an ɗauko shi ne kai tsaye daga littafin na Imam al-Maghili.)*

# SHUGABANCI DA FAFITIKAR YAKI DA CIN-HANCI

**1. Shugabanni Masu Gaskiya Ke Haifar Da Kyakkyawar Al'umma.**

Shugabanni tamkar marmaron ruwa ne, su kuma ma'aikata kamar laulawan ruwa ne. idan marmaron ruwa tsaftatacce ne ƙazantar laulawa ba za ta yi masa kome ba. Amma idan ruwan gurɓatacce ne, to tsaftar laulawa babu wani tasiri da za ta yi (ga kyawon ruwan)

*(Sarkin Musulmi Muhammad Bello, Usul al-Siyasa, Yamusa 2004: 11 da 16)*

**2. Haramcin Cin-Hanci Da Ayyukan Barna.**

An haramta wa shugaba da ya taɓa wata dukiyar da aka samu ta ƙamuya-muya, alal misali ta cin-hancin da aka samu domin naɗa alkali ko wani ma'aikaci. An yi ijima'i kacokam cewa amfani da irin wannan dukiya haramun ne. Tana lalata addinin, kuma ta buɗe wata wagegiyar ƙofa ga ɓarna, da kuma tursasa wa talakawa. Domin jami'an za su ji tunda an amshi kuɗi wajensu ladar ba su muƙamai, to su ma lallai su mayar da su daga jikin talaka.

Wani abu kuma wanda aka yarda cewa shi ma haramun ne, shi ne karɓar cin-hanci a madadin shugaba, ko wasu jami'ai kamar alƙalai da sauransu. Wato al'adar karɓar wani abu daga wajen daya daga cikin masu husuma ko dukkansu, ko dai kafin a yanke shari'a, ko bayan an yanke. Haka ma haramun ne a karɓi kyauta daga talakawa. Domin wannan hanya ce da za ta kai ga fitinu iri-iri. Idan kyauta ta iske mutumin da ke da iko, adalci da kyautatawa za su sami hanyar rabuwa da shi, kuma abin da ya yi shi ne ya sayo wa kansa muhalli a wuta.

*(Shehu Abdullahi Ibn Fodiyo, Diya'al Hakkam 1990:10)*

3. Fasadi A Kasar Hausa Ta Karni na sha Tara.

Ɗaya daga cikin hanyar mulkinsu ita ce gina ikonsu a kan abubuwa uku, Mutane, da mutuncinsu da kuma dukiyarsu, duk wanda suke so su kashe, ko su kora daga ƙasa ko su ci mutuncinsa, ko kuma su ci dukiyarsa, sai su yi domin biyan buƙatunsu ba tare da wata hujja a shari'a ba. Ɗaya daga cikin hanyar mulkinsu, ita ce aza wa mutane kudi wanda shari'a ba ta ce ba, irin wanda suke kira jangali, ko kudin gari ko kuɗin salla. Ɗaya daga cikin hanyar mulkinsu ita ce cin duk wani irin abinci da suke so da gangan, walau shari'a ta halarta ko ta haramta, da kuma sanya duk wani irin kaya suke so, Walau shari'a ta halasta ko ta haramta, da kuma shan duk wani abu da suke so walau shari'a ta halasta ko ta haramta, da kuma hawan duk wata dabba da suke so, Walau shari'a ta halasta ko ta haramta, da kuma żama da matan da suke so, ba tare da aure ba, da zama a cikin fadojin da aka yi wa kawa, da shimfiɗa dardumai masu laushi da kwalliya yadda suke so, walau sharia ta halasta ko ta haramta.

Ɗaya daga cikin hanyar mulkinsu, ita ce jinkirta biyan bashi wannan kuwa zalunci ne. Ɗaya daga cikin hanyar mulkinsu ita ce abin da sarkin kasuwa yake karɓa daga duk waɗanda suka yi hulɗar cinikayya, da kuma naman da yake karɓa daga rundawa a duk ranar kasuwa. Ɗaya daga cikin hanyar mulkinsu, wadda kuma wani abu ne sananne ita ce duk wanda ya rasu a ƙasarsu, za su ɗauki kayansa su kira shi 'gado', sun kuwa sani ko shakka babu cewa zalunci ne. Ɗaya daga cikin hanyar mulkinsu ita ce su aza haraji kan attajirai da sauran matafiya.

Ɗaya daga cikin hanyar mulkinsu, wadda kuma sananna ce, ita ce idan kana da wanda kuke shari'a, kuma ya riga ka wajensu ya ba su kuɗi, to ba za su karɓi batunka ba, duk kuwa da cewa sun san gaskiyarka,

sai fa idan ka ba su abin da ya fina abokin shari'arka. Ɗaya daga cikin hanyar mulkinsu ita ce su hana mabuƙaci ya gansu.

Ɗaya daga cikin hanyar mulkinsu, itace bayar da kyauta ga wanda ya yi masu iso ga mai mulki. Daya daga cikin hanyar mulkinsu ita ce ƙarya da zamba da girman kai. Ba za ka taba ganin wani daga cikinsu wanda baiji da kansa ba, kuma duk wani wanda ya nuna rashin girmama su ko ɗan yaya, za su hukunta shi a kan haka.

(Shehu Usman Ibn Fofiyo,*Kitaba al-Farq*, M. HIskett: 7-11)

### 4. Kyauta Ga Jami'an Gwamnati

Akwai hadisin Annabi a Sahih Buhari a a game da dokar da ta shafi kyaututtukan da ake ba su, cewa Annabi ya naɗa wani mutum mai suna Ibn Al-Lutbiyya a matsayin gwamna. Da mutumin ya dawo wajen Annabi, sai yace: "Ya Manzon Allah, wannan naka ne, wannan kuwa an ba ni ne kyauta." Sai Annabi ya ce, cikin fushi: "Ta yaya mutumin da muka ɗauka ya yi mana wani aiki zai ce. wannan naka ne, wannan kuwa an ba ni ne kyauta?" Mene ne ya sanya bai tsaya a gidan ubansa da uwarsa ba, ya gani idan za a aika masa da kyauta a can.?"

Malik ya ruwaito cewa Umar Ibn al-Khattab ya riƙa kwace rabin dukiyar gwamnoni. Idan ta bayyana cewa bayan ya naɗa su gwamnoni suna da dukiyar da wadda a da ba a san su da ita ba. Dalilin wannan kuwa shi ne koda yake abin da gwamna ya samu ba tare da an ba shi cin-hanci ba halal ne, to amma ba shi da hujjar amsarta, domin yana riƙe da babban mukami a matsayinsa na gwamna, kuma zai iya samun abin da wasu ba su iyawa ta halal. Saboda haka sai a zuba rarar dukiyarsa a baitul mali. Attab Usayd ya taba cewa. "Tsakani na da Allah abin da kawai na amfana daga aikin da Manzon Allah ya ba

ni shi ne riguna guda biyu, waɗanda naba yaro na (mai suna) Kaysan."

A cikin Shurb al-Zulal (bayan baitocin) an ce ka bar duk wani abu wanda shugaba ya amsa domin ya yi hukunci, ko da kuwa hukuncin daidai ne, kada Ka ci shi.

Sai ya ce:

*Kwatankwacin wannan ita ce kyautar da aka ba mai mulki, duk wannan haramtacciyar riba ce ta kuskure.*

(Shehu Usman Ibn Fodiyo, *Bayan Wujub al-Hijra*, El-Masri 1976: 74 -75)

Cikin irin wannan ruɗun shi ne akwai wasu mutane da suka ɗauki cin –hanci a matsayin 'kyauta'. Wannan ma kuskure ne kuma ruɗu a ijima. Domin an bayar da ma'anar 'kyauta' da cewa wani abu ne da aka bayar domin a ƙarfafa soyayya, alhali cin-hanci wani abu ne da aka bayar domin a rusa haƙƙi na halaƙ (na wani), ko kuma domin a samo abin da yake haram.

*(Shehu Usman Ibn Fodiyo, Hisa al-Afham, F.R. Siddiq 1989:125)*

**5. Sanya Ido A Kan Ma'aikatan Gwamnati**

Lallai dangantakar shugaba da ma'aikatansa ta zama kamar ta makiyayi a tsakiyar Mafaɗatan Zakoki, sune za su kula da mutanensa a madadinsa, shi kuma yana sanya ido a kansu. Duk wata ɓarna tana fitowa ne daga mugayen ma'aikata. Lallai shugaba ya binciki duk wani mutum wanda ake kyautata zaton sa ne da yin ɓarna, alal misali mutumin da shaidu na kwarai suka furta cewa an sami giya da wasu lalatattun mutane a gidansa lallai ya bincika zargin, idan gaskiya ne, ya hukunta wanda ake zargi, ya kuma yi maganin fasadi, ko kuma ya yi fushi dashi ya la'ance shi.

*(Shehu Abdullahi Ibn Fodiyo, Diya al-Hukkam, Yamusa, 1990:9)*

6. **Bayyana Dukiyar Da Aka Mallaka.**

Lallai shugaba ya zama yana son ya san hakiƙanin halin da ƙasa ke ciki domin son tabbatar da gaskiya ba domin kyashi da haɗama ba. Wannan ya shafi al'amarin ma'aikatansa, ta ƙoƙarin ya san halin da suke ciki, ta hanyar ƙirga dukiyarsu kafin ya naɗa su, da kuma sanya ido a ayyukansu lokaci-lokaci. Ya gargadi duk wanda ya a kasa aikinsa; ya kori waɗanda suka wuce-gona-da-iri, kuma ya maye gurbin duk wani wanda aka yi kuka da shi. Duk wanda aka samu yana da dukiya fiye da wadda ya samu a wajen aikinsa, to tilas ne shugaba ya amshe ta ya mayar da ita baitalmali. Idan an tabbatar da asalin dukiyar, to ya ƙwace rabinta daga ma'aikacin

*(Shehu Abdullahi ibn Fodiyo, Diya al-Hukkam, 1990:9)*

7. **Ba Sani- Ba- Sabo Da Ma'aikatansa.**

Dole ne shugaba ya zama ba-sani-ba-sabo a mu'amalarsa da ma'aikatansa da yaran gidansa. Za su iya yaudarar shugaba domin amfanin kansu. Su nuna masa yin zalunci daidai ne, ta haka kuwa sai su jefa shi a wuta, domin biyan buƙatunsu. Ba ka da babban maƙiyi tamkar mutumin da yake neman halakaka. Ma'aikata da yaran gida a ma fi yawan lokuta bayi ne na abinci da jima'i da sauran kananan bukatu, domin samun biyan bukatunsu. Irin waɗannan mutane suna iya amfani da shugabansu su biya bukatunsu, kuma ma ai aikinsu domin taimakon kansu ne, ba domin taimakonsa ba. Alamar wannan ita ce da zarar sun ji jita-jita cewa za a kori gwamnansu daga aiki, a maye gurbinsa da wani, dukkansu za su juya masa baya, su fara kamun-kafa ga wancan mutumin. Za su yi hidima a duk inda kuɗi suke kuma su miƙa wuya...

*(Sarkin Musulmi Muhammad Bello, Usul al-siyasa, Yamusa 2004:16)*

8. **Shawara Ga Ma'aikatan Hukuma.**

Ma'aikatanka da kai suke kdyi. Idan ka yi zalunci, sai ka zama tamkar dabbar da ta samu ciyawa ta ci ta batse har ta yi kiba. Sai kibarta ta zama sanadiyar halakarta, domin an yanke ta aka cinye domin kibar.
*(Sarkin Musulmi Muhammad Bello, Usul al-siyasa, Yamusa 2004.16).*

9. **Dukiyar Maɓarnatan Masu Mulki.**

Ka sani cewa ra'ayin malamai ya bambanta a kan batun dukiyar masu mulki. Wasu daga cikinsu sun ce "Babu wani abu da yake halal daga cikin dukiyarsu ko ga masu kudi ko ga talakawa, domin maɓarnata ne. kamuya-muya ta dabaibaye dukiyarsu. Dokar ta shafi ma fi yawan mutane. Saboda haka dole ne a guje ta". Wasu suka ce "Ta halasta ga masu kudI da talakawa idan mutum bai gane cewa ta haram ce ba hakkin na a kan mai bayarwa". Wasu kuma ("Ta halasta ga talakawa amma baga masu kudi ba".

Nace gaskiyar magana ita ce duk wata dukiya wadda aka san masu ita (ba tasu ce ba), to haram ce, a Ijima'in malamai, amma duk wata dukiyarsu wadda ba a san ta su wace ce (suka handame) ba, to halal ce a ra'ayin malamai Muhammad b. Abdul-Rahmann al-Barnawi ya fadi a wakarsa Shurb al-Zulal:

*Duk wani abu haramtacce, wanda kuma an san mai shi*
*Duk wata hanya ta samun shi ɓattata ce, ya dan'uwana*
*Sai dai idan an yi niyyar mayarwa tsakani da Allah*
*Ga Mai ita, idan haka ne dauki ba hamayya*
*Amma dukiyar da ba a san ta wace ce ba ita halas ce, an yarda a more ta.*

Na fada cewa abincin masu mulki halal ne idan mai nukewa (lalacewa) ne, kamar yadda fitaccen ra'ayi ya nuna. Ahmad al-

Zarruƙ yace. Wannan doka ce ta shari'a, haka kuma Muhammad b. Abd al-Rahman al-Barnawi ya faɗa a Shrub al-Zulal:

*Abinci mai nukewa na iya zama halal*
*A yadda fitacciyar doka ta nuna abokina*
*Kin amfani da shi taƙawa ce, kamar yadda doka ta ce.*
*Ga duk wanda zai iya guje wa*
*Abin da ake tababa (shubha) to ya guje shi.*

*(Shehu Usman Ibn Fodiyo, Amsar Shisummas, a cikin O. Bello & H.T. Norris, 2001:14)*

# KANURI VERSION

## FERNO NƏM WURABE (FOUNDATION OF LEADERSHIP)

### 1. Nəm Fuwuma Də Aman Alabe (leadership as God's trust)

Haiya maro shi kəntəwo siyasabe də kənjo kəmayeye kuru nəm kazalla nabi Alabeye nangadəro awo shiro hiwata'a də daraja'aye kuru zauro kuewowuye. Shi fuwumadə lai ngəla gowono'a daji dunya au awo dunyabero shim kazəjimba, amma dunyaro dunya gulwonda daji nəm adalnzədə zəwurin. Nanga dəro Ala-ritamaro walle (waneye nasartəmin). None naskuwoso sai kərmu sətambiya, kuru yim chinoo'a də kəla kundonəmbe wooson sai nya soworiya. Ndu duwo kundonzə ngəlawono yaye, sha zaumae sakkin, dalilzədə awo dunyabero zəktənyi dəyə səkkə.

### 2. Nəm fuwuma namtə sikkel jirebe (leadership as accountability)

Yaa harami, takne dea nəm fuwuma jamayee karəgə zauzə kura fal də shima jim jirebe awo dimma sammayen nya kulasta də. Ngaila dənna kənjiwoso kəla mana'anzə'a kundoanzəa halwanzeaben sha kushetin. Shila fuwuma jamabero walwono'a ngawo kəla kundonzəben sha kushezanabe man, kəla jamanzəbeyen sai sha soworiya. Daji kamdə halzə battiro walwono'a shi yawalnzə, dalilzədə awi sədə kəla hakku jamanzəben təmoyin? Adəma nangaro gultin, adu-do kəmandeye hakku jamabe dawunzəro lujiwo yaye, kəla hakku adəben sai sha tuworiya. Shi donyi lamar dunyabeye sha bəlezənyi adə sha gawurtin, amma adəgənyiya sai shiye njokkunotiya kəla kundoanzə diwi-diwiben

Adəma nanga Nawi Alabe (SAW) guljin nandiro kəla ndu fuwuma'a awo surodən dəgana'a gulge wa'o? (daji kərəntəwu soye a-aa ada) daji Nawi Alabe (SAW) ye gulwono "badiyaranzədə shirwu, kən indiminzə də chanongəna'a kən yakkəmidə azəbtə yim chinoo'abe"

Ali bin Abi Talib suro hadithzə al-jawhana yen guljin jim fal dina suwa fit Umar Bin Al-khattab kəla dabba kaskataben sha churukkonye chuworukko, yaa kura muminnaye ku ndara lenəmin wokkonya daji wono, kalima alangkaro sowodina fattəgəna mangin wono. Daji nge-gulwokko, halnəmbe fəlezəna nyi Ala-ritamaro.

Daji shiye wono wande ayauro rumi kam Muhammad'a sunotənadən kashi bukkəna, chi kənadugu sham yendo chim fal fatkatə yaya, yim chinoo'a Umar'a soworin, dalilzədə fuwuma jamanzəro chəssəngənyidə sha azəbtin dəro shauma ba wono.

### 3. Nəm fuwuma martawa'a (leadership as beneficence)

Faida nəm fuwuma jamabea kazəyi do surodən dəgana'a ɗə futu kingiyam Alabe (SAW) be guljn dən wono "fuwuma jamabee jirenzə kawu falye də, modua kamfalye saa fitulur (70yrs) yea kozəna" Nawi Alaye (SAW) guljin " kam təragənaye ala'a sha karəngəye də shima fuwuma donyi jiremadə, amma kuru kam Kəmandebe waazəna danodə shima fuwuma donyi shi adalgənyidə." Kuru Nawi Alabe (SAW) guljin "fuwuma jamaye kundonzə ngəla faldə, kundo ngəla jamanze duksobe'a tilowo wono" kuru mukkowa sala am dəwu fitulur (70,000) yea tilowo wono."

Daji adəgaimaro wallono'a ashi shim Alayen awo ardi'ata nəm fuwuma jamaye gai gullewe. Kuru na kəmandeyen kənda fuwuma jamaye loktu fal (one hour) ye də alama kam falye kənda ngəlinzəbe'a tilowo nangadəro ndu yaye kam hal adə kolzə lezə jama njokkunotəro gaiyaa shi wano kəmandeyero waljin dəro shaəma ba.

## 4. Nəm fuwuma jamaro chidatəbe (leadership as service to the people)

Kuru ndu donyi nem fuwuma jamaye dawunzəro lujiwo yaye, chidanzə'a Ala-ritalan sədə. Salaam taltə mbeji amma shi de alai gawurabe kurawo. Ndu duwo chidanzea Ala-ritalan kəlzə chido yaye, shaə-bamaro shi karəgə kəji'aye kuru haraiyero dəgai kuru donyi hakkunzəa Ala-rita baro sha sədiyaye, shə bamaro njokkunotinne kuru kəmandə'a sasəranyi gairo gotin. Guwuaro wallimiya dole jamaro njiskəmin. wande shi gumna sə affiso chidaanzəbedə ka'anzəro gozənyi; Ala affiyaye səragənaro shin, wazənaro dapchin adəgai gənyi. Hal jiri adə lai kolzənaye kuru nəm jahilro walzənaye. Nozə dea sha galatə adə jamaro chissəgə hakku jamaye cho dəmaro dea sha gala'ada.'

Jamaro njista'a falde duno bəriye dəwu faidatə'a kozəna dea. Dea wande njassənyende, nzando kərmaibedə shima himmanzə gai, jiren naptagai, kuru nəlefa jamanzəyero chinəm datəgai shima dea razəgənzəye danowo. Nduma lai koltəlan fuwujinba, nduma taljinba ba, kuru duwun soye ba.

## 5. Nem fuwuma namtə diyel jireba (leadership as Justice)

Fuwuma ndaraye yaye kam kəla kəladoanzəben nasartəna rumiya jamanzə'a jiren rozəna; kuru ndu do sha ruzana ruwiya shi jirenzə ba. Fuwuma wroso karwaramzə də jire'a hal-ngəla'a. ndu yayero jirenzə tawattsəgə jire adə na nduyendo səmon kam dəro chin yaye kal. Kuru hal ngəla dəye jama soro liwunzən butu luwu bana sədə, wande baitəmbal jamayen gozənyi, kuru am indi kambiita fuwunzəro lizaiya, ngəllaro suru, nozoru sədə ritəso, gotəgəso baro jiremaro jirenzə tawattsəgə. Ndu do lezə sha adujiya wande sadən fəska kolzənyi, wande chilan suluwunyi, sais a jiremadə asujiya allando ja'awu jirebe kalaktsəgə. Fuwuma jamabe də sambisoro dawu jamanzəyelan naptsə,

kamu'a, duli'a samma sha sorus. Kuru am galagalazəna alama sharaso chidawu soro affiso wande kolzənyi, Dalilzədə burwuwa laa də waneye kəla am galazəna anyiyenno waljin nangadəro loktu loktulan chi jamaye kərənzə jiremaro jirenzə cho. Hatta sawaa Nawi (SAW) soma am galazana soa sosotuluwuna kəla burwu jama mewuyen. Dalilzədə shi nəm ngəla adə shima zar kərmaibewo, nəm ben-nzədə isə nəm diwi bəl-fokro waljin nangadəro shi sambisoro kənasar na Alayen kənandeye gulzəna-Ala de kundo kəladoabe sodəyea nozəna sai lejin jirebero sandi'a wujuwo.

Diya al-khulafa ye guljindən wono: shi shi luwuran adə kam njokkunoma dəa shi njokkuno'ata dəa duksoro ishara təngər sədəna wono. Ka'ab ye yim fal Abu Huraira ro guljin Ala-torah ye gulzəna: fato njokkunomaye də wurtin; kuru Qur'an kambo yee tawotsəgəna. Ibn Abbas yee guljin rasulu (SAW) guljin "wande kam njokkuno'ataro riskəwi dalilzədə sandi Ala'a ma dea karəngəwo". Ndu yaye kam kamanzə njokkunozəna də datelaman gawara mazə dalilzədə yim dinarso, kungunasoye faljinba ishin dea wono. Yim adəadə halzə ngəla-ngəla duk samou kam njokkuno'ataro sadiin, shima halzə ngəla-ngəla ba'a ayauwa kam njokkuno'atabe də shiro kalaktsain. Kuru Sa'id b Zayd guljin Nawi Alaye (SAW) gulzo wono "ndu duwo chidi gana kamma dolen chimowo yaye, yim jjirebe na shima dəa chapcha tulur-ro sadə dawunzəro kolzain "Anas ye guljin Nawi Alaye (SAW) gulzo: Yanəmgana'a banana, shima njokkunomawo au njokkunoa'ata yaye" Daji chuworo yaa Nawi Alaye (SAW) gəle shi njokkuno'ata dəye gənyi shi njokkunotəna dəye wa wanonya, Nawi Alaye (SAW) yo aa! Shi njokkunotəna dəadaptəmau wono, Bilal b Sa'ad yee guljin Alaro rinəmiya kam Ala-taskomayero rine wono. Nawi Alaye (SAW) guljin kəmande gulzo wono kam wa Ala dəgənyiya gəratəgəramzə gadə ba'a njokkunojin dəro gəra'akin wono. Nawi Alaye (SAW) guljin "ndu yaye kam

watəma indiye katero gaə jire gana sədiya kəmandeye sha lanjin wono" Kuru Nawi Alaye (SAW) guljin yum laira waajiya, am yakkə (3) də Kəmandeye sandiya kalaktəma surinba wono: kura do kattuma'a, kamkura do shirkama'a kuru kam muskodea do kəlanzə awashinna. Kuru Nawi Alaye (SAW) sawaanzəsoro guljjin, "yim ishinna mbeji yimdonyigədia'a fəte'a samma kərigənən buwi, kuru sandi samma rokkondonno walzai, saide am kurissa jamaye gozanaso sandima kannuro tamin. Saide am Alaro rizanamaso sandima gawutain, dalilzədə lai sak zaa hakkunza'a jirelan kəlanzalan sasagənamaso sandima Zannaro tamin wono.

Kuru Nawi Alaye (SAW) guljin ndu duwo fuwuma jambero walzə, jamanzəa hariptsə, sandiro hakkunza daptsəyi yaye au kanjimoli ba'aro waljiyaye zannaro gayinba wono. Kuru waltə gulwono "ndu duwo hakku mushimmaue mukkonzəro saakke do alama kəntanzə faijingairo sandiya faitəro waajiyaye shaə bamaro konnuro gayin. Kuru Nawi Alaye (SAW) guljin "suro wumma'anyiyen am indi rahma sawandinba wono-fuwuma jamaye do jirebaa'a, kam kuru kaiya luwuranne fanjinba ngal kojinna. Kuru kam donyi yim jireyea sha njokkunozaidə ffuwuma jama kam kanjimoli ba'a də".

## 6. Hal-ngəla shima ferno nəm fuwuma jamayeo (leadership as goodness)

Shi nəm ngəla adə alama kazəmu hal taasanave gai. Tənda Kəmande Alaye nozəna, nduso gənyi jiren naptalan fuwujin adəgai, shih al ngəla dəye yaana jirebe nanga dəro Kəmande am indisoa karramzəna. Dukshi manadəyedə, am sana yakkə soa lezəna:-kam kura'a, gana'a dawu-dawu'a. daji fuwuma də kam kuradən namtə babayen səta, dawu-dawuye dəa namtə ya'anaben səta, ganama dəa namtə tadaben səta nangadəro hakki babanye kəlanzən səsagə, yanzaanaro bana sədə tadanzəa sasabtsəgə.

**7. Nəm fuwuma namtə ferno nəm ngalwobe (leadership as cultivation of excellence)**

Shi kəmandebe jamaro chəkkərawo'a sandiro fuwuma ngəla galazənyin kuru am sandiya banatəwuye chin, fuwuma jili anyi jamanza'a zawal saklan sonotinne, lamarranza'a kakkalro sonotinne. Sanbisoro shawari hangalwuye gozai kəla kazəyi jamanzaye galtəyen. Amma kəntəwo'a kəntəwoa'a, hangalwu'a am kamba'ata goza fella fella woson bana ləatarza sadin. Kuru modua salihhayeye mazai kəla jama sodə kəaye lai-kanəmbe lai lan dasawuyen. Am jili anyi, am donyi darajanza haptaasandəna soa haptsa;a kuru am nadəro nazaanyi soye nanza kakkallan gənazai.

**8. Nəm fuwuma jamaye namtə kurita hangalye (leadership as moral responsibility)**

